

DEREK PRINCE
MINISTRIES INTERNATIONAL

Abincin Yini

Yarda da Kanmu

Yesu ya ɗauki ƙiyayyar mu domin mu sami amincewar Sa a wurin Uba



Furta Kalmar Allah
Daga Derek Prince

Ta wurin aikin bangaskiya, dole ne ka yarda da abin da Allah ya faɗa a cikin Littafi Mai Tsarki: cewa an karɓe ka cikin Kristi. Littafi Mai Tsarki ya gaya mana cewa nufin Allah tun fil azal shi ne ya mai da mu 'ya'yan Sa, Ya kuma cika wannan manufar, Ya sa hakan ta yiwu, ta wurin mutuwar Yesu a kan gicciye a madadinmu (dubi Afisawa 1:4–6). Idan ka zo wurin Allah ta wurin Yesu, Allah zai karɓe ka. Ba zai kore ka ba.

Domin ɗaukar wannan mataki na samun karɓuwa, dole ne ka yarda da kanka. Sau da yawa, wannan shi ne abu mafi wahala a gare mu mu yi. Mukan dubi tarihin gazawa da ƙaryar da aka fara da ita, wataƙila da kuma hanyoyin da muka kasa wa waɗansu. Kana iya ɗaukar kanka "kasasshe," amma Allah ya ɗauke ka "Ɗana" ko "Ɗiyata." Dole ne mu yarda da kanmu domin Allah ya karɓe mu.

Idan ka zo wurin Allah ta wurin Yesu, kai sabon halitta ne:

> "Saboda haka, duk wanda yake cikin Kristi, sabuwar halitta ne; tsofoffin al'amura duk sun shuɗe; ga shi, sun zama sababbi. Duk wannan kuwa yin Allah ne, shi da ya sulhunta mu da kansa ta wurin Yesu Kristi" (2 Korintiyawa 5:17–18)

Wannan ita ce sabuwar halitta. Kada ka yi tunanin kanka game da yadda ka ke kafin ka zo wurin Kristi, domin ka zama sabon halitta.

Bari mu yi addu'a tare: "Allah, Na gode maka da ka ƙaunace ni, ka ba da Yesu, Ɗanka, ya mutu a madadina. Na gode maka domin ya ɗauki zunubai na, ya ɗauki ƙiyayyata, ya kuma biya hukuncina. Kuma saboda na zo gare ka ta wurin Sa, ba ka ƙi ni ba, ba ka ce ba ka so na ba, ba ka ware ni ba. Kana ƙaunata sosai. Hakika ni ɗanka ne. Kai Ubana ne da gaske. Ina cikin iyalin Ka. Sama ne gidana. Na gode maka, Allah. Amin."

Na gode maka, Yesu, saboda aikin ka a kan gicciye. Na gaskata abin da Allah ya ce—cewa an karɓe ni cikin Kristi—kuma na yarda da kaina ma. Ina furta cewa Yesu ya dauki ƙiyayyata domin in sami amincewar Sa a wurin Uba. Amin.

© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.

Abincin Yini ★

Kwafi: WD-B097-146-HAU

Sabuntawa ta ƙarshe: 24 Sept 2026

Yanar Gizo: Derekprince.com/ha/resources



© 2008 - Derek Prince Ministries, International, Inc.